# Jawabi A Majalisar Hukumar Taron Harkokin Kasuwancin Amirka da Afrika Da Ake Yi Sau Biyu A Shekara

**Hillary Rodham Clinton**
*Sakatariyar Gwamnatin Amirka*
**Cibiyar Taro Ta Birnin Washington**
**Birnin Washington, DC**
**1 ga watan Oktobar 2009**




Godiya na ke yi. Na gode Stephen, kuma ina mai alfaharin halartar wannan wurin, don bayar da gudunmawata ga wannan muhimmin shirin. Ina yi ma ku godiya tare da Majalisar Hukumar Afrika, a kan matuƙar ƙoƙarin da kuke yi, na ƙarfafa dangantakar harkokin ciniki da kasuwancin dake tsakanin Amirka da ƙasashen Afrika. Ina kuma bukatar gabatar da takwarana, a wannan gwamnati, mai wakiltar Amirka a Harkokin Kasuwanci Ambassador Ron Kirk, wanda babban mai bayar da shawara ne, waje inganta harkokin tattalin arziki da faɗaɗa harkokin kasuwanci. (*Sai aka runtime da tafi).*

To, kamar yadda Stephen ya ce, na yi wani gwauron tattaki, a cikin watan Augusta, kuma na ziyarci waɗansu wurare, da ban taɓa zuwa ba, na kuma je waɗansu wuraren da na sani. Amma, maƙasudin wannan rangadi, shi ne, a san muhimmancin Afrika ga Gwamnatin Obama. Babu shakka, ni kaina ina ƙaunar hakan, amma, a tahaƙiƙanin gaskiya, gwamnati kanta, ta fi mu damuwa da wannan, domin tunaninmu ne cewa, ci gaba da wadatarmu ta tahallaƙa da makomar Afrika. Kuma Gwamnatin Obama ta ɓullo da waɗansu dabarun taimaka wa bunƙasar tattalin arzikin Yankin Yammacin Saharar Afrika da kuma tattalin harkokin da za su kyautata halin rayuwar jama'ar Afrika, wanda mu, a gare mu, ya danganta ne da irin nasarorin da kuka samu. Tuni, mun manta da irin yadda ake kallon Afrika, a matsayin ƙasar dake fama da talauci, cututtuka da dai sauransu. Za mu kuma ci gaba da gina ƙwaƙƙwaran harsashin sababin harkokin dangantaka da Afrika, irin wanda za mu yi cuɗanyar amfanar juna da haɗin gwiwar da zai kawo mana alfanu, mai jurewa.

Daga irin tunanin da muke da shi, tun ba yau ba, ana yi Afrika kallon almajira, maimakon lura da irin albarkatun da take da su, waɗanda ke da ƙarfin sarrafa tattalin arzikin duniya a Karni na 21. Don haka, lokaci ya yi, da za canja

wannan tunanin. Lokaci ne da za a mayar da hankali ga ƙarfafa harkokin cinikin da za su bunƙasa kasuwannin da muke da su, har su faɗaɗa. Lokaci ne da harkokin fasaha ƙirƙira za su sanya ƙasashen Afrika su yi tashin gwauron zabon magance duk wani mummunan yanayin harkokin ci gaban da za su hanzarta cuɗanya da kasuwannin duniya. Lokacin ne kuma da za a bayar da himma ga sake fasalin harkokin noma, don ci gaban makoma da wadatar Afrika, da kuma kyautata halin rayuwar jama'arta, musamman mata. Wannan shi zai hanzarta ciyar da Afrika gaba, domin kai wa ga biyan bukatar da muke nema.

Yanzu muna da ƙuduri babba, kuma ga alama akwai haske. Amma, dole mu lura cewa, babu wani abin da zai wakama, ba tare da mun inganta harkokin shugabancin Afrika ba, ko gudanar da gwamnatoci masu adalci da nuna gaskiya, tare da mutunta dokoki, da yi wa jama'a aiki, da kuma kula da yin amfani da dukiyar ƙasa, da girmama 'yancin ɗan adam, da kawo ƙarshen cin hanci da rashawa, wanda ta yi mana katutu, a zukata da harkokin kasuwancin miliyoyin jama'a. *(Aka runtume da tafi).*

Yanzu kuma mun san cewa, akwai shingaye a gabanmu, amma a shirye muke da haɗa hannu da ku, wajen samun nasarar abinda muka sa a gabanmu. Na yi farin cikin ganin Shugaba Kagame a wurin nan, domin duk da irin talaucin da ya so abka wa duniya, Kasar Rwanda babu abinda ya same ta, tunda tattalin arzikinta ya ci gaba da bunƙasa, wannan kuma ba zai rasa nasaba da ƙwararan manufofin gwamnati ba, da ake aiwatarwa. Lalle ya kamata mu yi ma ta guɗa. (Aka runtume da tafi).

A dukkan ƙasashe bakwan da na ziyarta, na ga ayyuka da harkokin kasuwancin dake da alfanu, na ga harkokin binciken kimiyya a Kenya, waɗanda a yau ke amfani da dabarun noma, na zamani, wajen kyautata iri, da taki da kayayyakin noman dake raya yankunan karkara. Kananan 'yan kasuwa a Kasar Afrika ta Kudu, sun duƙufa ga harkokin kasuwanci da buɗe kasuwannin dake gogayya da takwarorinsu na ko'ina a duniya.

A Angola kuma, na ga haɗin gwiwar dake tsakanin gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu, game da sababbin manufofin taimaka wa juna, da ƙwarewa a kan harkokin kiwon lafiya, a Jumhuriyar Congo, a inda suke sadaukar da raywarsu, domin ceto waɗanda bala'in tashin hankali ya abka wa, su kuma ƙungiyoyi masu zaman kansu, a Nijeriya, na ta fafitikar ganin an yi gyara ga dokokin zaɓe, da magance cin hanci da rashawa, yayinda ma'aikata a Kasar Liberia ke ƙoƙarin gina mulkin demokraɗiyya, ga ƙasa irin ta su, daga nemi wargajewa, wadda ta shafe shekaru tana yaƙin basasa. Su kuma shugabannin Kasar Cape Verde sun haƙiƙance a kan tabbatar da mulkin adalci da nuna

gaskiya, kazalika da inganta hukumomin da za su ɗaukaka tattalin arzikin wannan ƙaramar, a cikin ɗan ƙaramin lokaci.

Idan aka duba wannan zagaye da aka yi a Afrika, dole a san cewa akwai alfanun da za a samu, kuma akwai jama'ar dake iya wannan aikin. Amma, babu abinda ya rage illa mu taimaka ga tanadin damar yin haka. Don haka muke da ƙudurin abubuwa biyar. Na farko dai shine harkar ciniki. Mune muka fi kowace ƙasa hulɗa da Afrika. A wajen taron Hukumar AGOA, a Birnin Nairobi, na bayyana cewa, Amirka na haƙilon bunƙasa damar da ta samu, ta gudanar da harkokin kasuwanci, a ƙarƙashin Shirin AGOA. Muna son gina babbar harkar kasuwanci a Afrika, da taimaka wa masana'antu da ƙara ƙulla dangantaka, irin wadda na sanya wa hannu, lokacin da na je Kasar Mauritius.

Amma, dole, mu shawo kan jama'ar Afrika da su riƙa yin kasuwanci da junansu, ba tare da la'akari da kan iyakokinsu ba. *(Aka runtume da tafi).* Hakika idan jama'ar Afrika suka ƙulla yarjejeniyar hulɗar kasuwanci da junansu, za su samu arzikin ƙasa, mai ɗimbin yawar da ba su zato, maimakon hulɗarsu da ƙasashen Turai da Amirka. Don haka burinmu ne da mu janyo ra'ayin abokanmu, da ku bɗe wa junanku kasuwanni. *(Aka runtume da tafi).*

Na biyu kuma shine ci gaban ƙasa. Ba za mu manta da bukatunmu ba, kuma Gwamnatin Obama ta yi alkawarin ruɓanya taimakon da take bayarwa, nan da shekarar 2014, domin mun yi imanin ci gaban ƙasa ne, kan gaba, a haɓakar tattalin arzikin duniya. Amma, mu za mu canja salo. Mu za mu mayar da hankali ne ga kafa ƙwaƙƙwaran ginshiƙin da ba zai bautar da wata ƙasa ba. (Aka runtume da tafi).

Za mu mayar da hankali ne ga shirye-shiryen kowace ƙasa da kuma irin yadda take inganta harkokin tanadin abinci da tsaro da abubuwan inganta harkokin rayuwa da muka mata. Za mu, kuma, mayar da hankali kan tsimi da tanadin kowane ƙasar dake hanƙoron kawar da cin hanci da rashawa da kuma gudana da mulkin adalci. Za mu kuma yi ƙoƙarin inganta raya yankunan karkara, a cikin ruwan sanyi, domin magance matsalolin da muke fuskanta.

A Taron Magance Gurɓacewr Duniya na Clinton, a Majalisar Ɗinkin Duniya, da aka yi a Birnin New York, na fayyace sababbin manufofinmu na magance yunwa da sake fasalin harkokin noma a duniya. Tanadin abinci, na cikin irin abubuwan da waɗansunku ba kulawa, amma yana da muhimmanci ga nahiyar Afrika. Tattalin arzikin nahiyar ya ta'allaƙa ne ga aikin noma, kuma kashi 70 daga cikin 100 na manoman afrika, mata ne, waɗanda aka mayar saniyar-ware, waɗanda ba a taimaka wa, wajen inganta harkokin noma abincin da suke

bukata, wanda da wuya suke samun isasshen abincin da za su kai kasuwanni, su sayar.

Bunƙasa noma da inganta noman zamani, ya yi komai amfani da sauƙi a Afrika, kuma ina kira ga dukan wanda ke sana'ar noma, da haɗa kai da mu da Cikakken Shirin Bunƙasa Harkokin Noma, a Afrika, wanda ke da kyakkyawan amfani. Dukan ƙasashen duniya, sun yi alkawarin bayar da kashi goma cikin 100 na kasafin kuɗinsu don bunƙasa harkar noma.

Game da haka, ne Kasar Rwanda ta yi zarra. Ita ce ƙasa ta farko da ta kammala dukan shirye-shiryen inganta harkokin noma, kuma ga shi tana cin ribar al'amarin. A cikin shekaru uku, Kasar Rwanda ta ruɓanya kuɗin da take kashewa, a kan aikin noma, har sau biyar, ta kuma ruɓanya albarkar abincin da take nomawa.

Don haka tanadin abinci ba sai don a taimaka wa waɗanda fari ya shafa ba ne. Yana magance dukan manyan matsalolin da yin illa ga ci gaban tattalin arziki. Shi ya sanya Kungiyar Kasashe Takwas Masu Arziki (G8), da Kasar Italiya, suka yi alkawarin bayar da dolar Amirka miliyan dubu 20, don tanadin abinci. Mu ma, mun yi alkawarin bayar da dolar Amirka miliyan dubu uku da miliyan 500, ga namu shirin, a cikin shekaru uku.

A duk lokacin da muke tunanin tanadin abinci da aikin noma, sai ɗawainiyar ta yi ta ƙaruwa. A dalilin albarkar dake wannan ɓangaren, dole mu mayar da harkokin nomanmu na zamani, mu kuma shirya kayayyakin gudanar da shi. Nan ba da daɗewa ba, na tambayi wani masanin harkokin Afrika game da irin abubuwan da nahiyar ke bukata. Amsar da ya faɗa ita ce: "Abubuwa uku ne, hanyoyi, hanyoyi, hanyoyi da kuma hanyoyi". Idan aka duba sai a ga cewa, muna ta binciken a kan dabarun da za su inganta kayayyakin aiki da kuma ƙwaƙƙwarar masaniya, da jari da kuma horarwa.

Ya kamata har ila yau, mu bincika al'amarin zirga-zirgar jiragen sama. Wa mai jawabi, a wajen Shirin na AGOA, ya bayyana cewa, abu mai sauƙi ne mutum ya tashi daga Birnin Nairobi zuwa London ko New Delhi zuwa Kinshasa ko Abuja, da ya yi zirga-zirga a tsakanin biranen Afrikan. Muddin ba mu tanadi yadda za mu kyautata zirga-zirgar jiragen sama, a filayen jirage ba, kamar yadda muke yi da gwamnatocin Liberia da Angola da Kenya, to, da wuya mu kai ga biyan bukatar bunƙasar tattalin arziki.

Haka kuma mun mayar da hankali ga Kalubalen da Karnin nan ke yi wa Hukumomi, a ƙasashen Afrika. Kamar makonni biyu da suka wuce, mun sanya

hannu, a kan yarjejeniyar dolar Amirka miliyan 540, domin taimaka wa ƙasar gyara harkokin sufuri da noman rani.

Ginshiƙi na uku shine tanadin abin makamashi. Afrika na da muuhimmanci waen tanadin makamashi, ba ga Amirka kaɗai ba, har ga duniya baki ɗaya, ga shi kuma ƙasashe masu arzikin makamashi, sai ƙaruwa suke yi. Na yi wata ganawa, mai muhimmanci, a Angola, wadda za ta haifar da ƙulla yarjejeniyar tsakanin ƙungiyoyi da dama, game da samar da hanyoyin samun makamashi da harkokin tsaro da aikin noma da abinci, kazalika da ƙulla yarjejeniyar yadda za mu tinkari al'amarin.

Bugu da ƙari na samu da shugabannin Nijeriya, mun kuma jaddada ƙoƙarinmu na haɗa gwiwa da Nijeriya,a fannoni irin sake fasalin dokokin zaɓe, da magance cin hanci da rashawa, da kula da harajin gurɓataccen mai, da ƙoƙarin samo sababbin hanyoyin tattalin arziki, kazalika da sulhunta tashin hankali, a Yankin Niger Delta. Kwanan nan, zan tuntuɓi kamfanonin haƙar mai, dake yankin na Niger Delta, don sanin irin abinda za mu iya yi, domin sake saka jama'ar Yankin Niger Delta, cikin ayyukan haƙar makamashin.

Ba shakka, idan ka kalli Nijeriya, sai ka tausaya ma ta. Kullum yawan jama'arta ƙaruwa yake yi. Jama'ar kuma dake fama da rashin abinci da rashin lafiya, sai ƙaruwa suke yi. Amma, me ya sa? Ba yin amfani da kuɗin da ake samu, yadda ya kamata, kuma a matsayinta na babbar ƙasar dake da arzikin makamashi, babu wani abin a-zo-a-gani, game da kyautata rayuwar jama'ar Nijeriya.

Yanzu muna taimaka wa Nijeriya da Angola da sauran ƙasashen dake da arzikin makamashi, da su riƙa kyautata yin amfani da dukiyoyinsu, su guje wa fatarar da za ta saka nahiyar cikin halin ƙaƙa-ni-ka-yi. Tuni ma, har gwamnatinmu ta fara wani abun. Na samo wani ƙwararre, David Goldwyn, don zama Babban Jami'in Hukumar Tafiyar da Harkokin Makamashi ta Duniya, don ci gaba da aiki da ƙasashen dake hulɗa da mu. Za mu taimaka wa sababbin ƙasashen da suka samu makamashi, da su kyautata yin amfani da dukiyoyinsu, domin kauce wa matsalolin da sababbin ƙasashen da suka samu mai da iskar gas da ma'adinai suke fuskanta.

A ƙarshe, muna masu farin cikin bayar da gudunmar dolar Amirka miliya shida ga Asusun Agaji na Bankin Duniya, don Kula da Kyautata Harkokin Masana'antu. Mun yi imanin kasuwanci da tattalin arziki na iya bunƙasa, a nahiyar Afrika, a cikin ɗan tsakanin da muka yi hasashe, kuma ta zama babbar mai haƙowa da sayar da makamashi.

Abu, na huɗu, da muke bukata shine haɗa dangantaka tsakanin gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu. Kamar shekaru 50 da suka wuce, kusan kashi 70 daga cikin na kuɗin da gwamnatin Amirka, ke bai wa ƙasashe masu tasowa, kyauta ne, amma a yau, kashi 80 daga cikin 100, suna fitowa ne daga hukumomi masu zaman kansu.

Bukatarmu ita ce, mu tallafa wa duk wanda muka gani yana da ƙwazo, a gwamnati, ko harkar kasuwanci, ko ƙungiya, kamar Kungiyar CCA da ƙungiyoyin jama'a. A ƙarƙashin jagorancin Ambassador Elizabeth Bagley, wadda ta shugaban ofishinmu na hulɗa tsakanin gwamnati da hukumomi masu zaman kansu, a duniya, mun bayyana sababbin hanyoyin hulɗa, ciki kuwa har da kawo Hukumar USAID da Asusun Rockefeller da Hukumar Kulle-ƙullen Harkokin Zuba Jari ta Duniya da Kamfanin JP Morgan Chase, su taimaka wajen bunƙasa harkokin dabarun dake da amfani a duniya. Muna ƙoƙarin binciko abubuwan da za mu yi, na alheri, ta hannun gwamnatoci, amma idan mun yi, wace rawa kamfanoni masu zaman kansu za su yi, ba don rimma wata riba ba.

Abu na biyar, mai yiwuwa, shi ya fi muhimmanci. A kullum muke ƙara jaddada shugabancin adalci da tabbatar da gaskiya, da magance cin hanci da rashawa da bin dokoki. Ba sai na faɗa ma ku cewa samun nasarar duk wata dama ba, sai da kyakkyawan shirin inganta harkokin zuba jari da kasuwanci.

Babu wani kamfanin da zai tinkari ragguwa ko haramtattar gwamnati, ko wurin da ake tashin hankali da aikata laifuka, ko cin hanci da karɓar rashawar da za su dagula ma sa harkoki da manufofi, ko kuma ƙasashen dake keta haƙƙin ɗan adam, ko cin mutuncin mata da budurwowi, ba kama hannun yaro.

Kasar Afrika ta Kudu, abin misali ce, a kan kiyaye haƙƙoƙin dake tsakanin mulkin adalci da bunƙasa tattalin arziki. Afrika ta Kudu, ta ƙwato kanta daga mulkin mallaka, ta tsoma jama'arta ga tafarkin mulkin demokraiyya, wanda ya sa ta zama akalar tattalin arzikin nahiyar Afrika. Kuma kamar yadda Stephen ne ya ce, kafuwar Hukumar Kasuwancin Amirka da Afrika ta Kudu, wata alama ce ta niyyar Amirka na matsar abokan hulɗarta dake Afrika ta Kudu.

Yanzu ne Hukumar Kula da Kyautata Harkokin Masana'antu ke da muhimmancin da za mu kawo ɗauki, haka kuma za mu inganta tilasta bin umurnin dokoki, ta hanyar horar da hafsoshi. Ina kuma mai farin cikin ganin yadda Hukumar Tsaro ta Majalisar Ɗinkin Duniya ta zartar da batun game da rashin nuna bambanci tsakanin mace da namiji, da al'amarin faɗe, wanda ita Majalisar ta Ɗinkin Duniya za ta yanke hukunci, a kai.

Akwai sauran aiki a gabanmu, amma irin nasarorin da za a samu, na ƙara mi ni ƙwarin gwiwa. Sai mu shekare, muna lissafin irin waɗannan abubuwan, domin duniyar nan na da faɗi. Amma na yi imanin babu yankin dake da ƙarfin yin haka, irin Afrika. Amma ba wai (aka runtume da tafi) za darashe ba ne, hakan ta faru. Dole sai mun haɗa ƙarfi, wuri guda.

Lokacin da na je Babban Zauren Jami'ar Nairobi, wata babbar ƙawata, wadda kuma ke fafitikar a kan tsabtar muhalli da kwanciyar hankali, kuma wadda ta samu lambar yabo, ta duniya, Wangari Maathai, na zaune tare da ni, a cikin jama'a, ta faɗi wani abinda ya ratsa mi ni ƙahon zuciya, da na ke ta bayyanawa, a faɗin Afrika cewa: "Afrika na arziki. Allolinmu na ƙaunarmu, lokacin da suka gina duniyarmu, amma duk da haka, muna cikin talauci".

Al'amarin akwai takaici, tun daga lokacin mulkin mallaka, har ya zuwa fitar ƙanginsa, arzikin nahiyar ke hannun waɗansu 'yan ƙalilan. Amma Afrika na da wata baiwar da nake bukatar kowa ya samu, musamman ku dake gwamnati da waɗanda ke kasuwanci, wanda wani shiri ne da Kasar Botswana ta yi, na haƙa da sayar da lu'ulunta ga Kamfanin De Beers.

Shekaru 60 zuwa 70, kafin ta samu mulkin kai, Gwamnatin Botswana ta yi tunani. Shugabanninta, a lokacin, sun sadaukar da kawunansu ga gina ƙasar da jama'arta za su samu gabala, idan mulkin mallaka ya kau. Sai suka fara yarjejeniyar kafa wata gidauniya, mai muhimmanci, wadda wani ɓangare na arzikin lu'ulu'unta, zai riƙa shiga asusun gidauniyar. Da kuma waɗannan kuɗaɗen aka shimfiɗa hanyoyi. Idan kuma ka je Botswana, za ka san cewa babu ƙasar da ta fi ta kyawon hanyoyi, sai dai kuma ko Afrika ta Kudu. Kuma shekara da shekaru mun ga fa'idar abin.

Ran nan na samu wasiƙar Shugaban Kamfanin De Beers, Mista Oppenheimer, inda yake cewa, "Muna godiya da ki ka bayyana dangantakarmu da Kasar Botswana. Mun samu walwalar gudanar da harkokin kasuwanci". Hakika, za ka iya gaggauta samun ribar da za ta amfane ka, idan ka yi haƙuri. Amma kishiyar haka Botswana ta yi. Don haka ku yi koyi da ita. *(aka runtume da tafi).*

Bari kuma, a ƙarshe, in ce a shirye muke da mu taimaka. Za mu taimaka wa abokanmu dake Afrika. Za mu taimaka wa ɓangarorin kasuwancin Amirka. Za mu kuma waiwaya ayyukan gwamnatocin da suka gabata, don ganin Gwamnatin Obama ta bambanta a Afrika, kuma muna ganin alfanun al'amarin. (aka runtume da tafi). Ba wai muna son yin hakan ba ne, ko kuma muna da dabarar yin haka, a'a, sai don wannan al'amarin yana cikin jinin Shugaba Obama. A kullum shi mutumin Afrika ne, saboda ɓangaren mahaifinsa. Ni, da shi, kullum muna tantaunawa ne, game da yadda za a kawo canjin dake bukatar

zurfin tunani da aiki tuƙuru da kuma irin hanƙoron da jama'ar Afrika ke da shi.
Don haka, mu tabbatar da gwamnatocin Afrika na kula da jama'arsu.
Na gode ƙwarai da gaske. (aka runtume da tafi).